**[1]Rahmatu Abdullahi Maiyaki da [2]Sanusi Gambo Bello, da [3]Lawi Yusuf**
[1]Department of Hausa, College of Education Zing, Taraba State.
[2]Bayero University, Kano
[3]Department of Languages and Linguistics, University of Maiduguri, Borno State, Nigeria

# Nazarin Halaye da Ɗabi’un Mutane a cikin Waƙar *Kalar Rayuwa* ta Sadiq Abubakar Bello

**Tsakure**

Ganin yadda kuɗi ya zamo abin soyuwa fiye da kima a wurin akasarin al’ummarmu a wannan zamani, wasu kan ma sun ɗauke shi tamkar abin bauta duba da yadda suke nemansa ko ta halin ƙaƙa domin su tara ko da ba za su ci ba. Wannan takarda ta yi ƙoƙarin zaƙulo tare da yin nazarin halaye da ɗabi’un mutane a kan lamarin kuɗi da kuma yanayin da suke shiga sakamakon rashinsa da kuma ire-iren ɗabi’un da suke nunawa wurin nemansa. An ɗora wannan aiki ne a kan Ra'in Zahiranciwanda yake la'akari da halayen zahiri a cikin litattafan hira da na wasan kwaikwayo/fim da kuma waƙa, wajen fito da wasu halayyar rayuwa na mutane a cikin al'umma na zahiri. A cikin wannan takarda, an yi ƙoƙarin nazarin halayyar ɗan Adam a cikin waƙar Kalar Rayuwa ta Sadiq Abubakar Bello. An yi amfani da fasalin sharhantaccen bincike (Discriptive Analysis) ne wurin tsettsefe bayanin binciken. Nazarin ya gano cewa mawaƙin ya yi ƙoƙarin bayyana wasu munanan halayyar ɗan Adam ta fuskar ɗabi’a da kuma yanayi a cikin waƙarsa da suka haɗa da gaggawa da zargi da kwaɗayi da rashi da son zuciya da ɓarna da butulci da tozarci da haɗama da yaudara da rashin tabbas da kuma jarabce-jarabcen da ɗan Adam ke shiga wurin neman kuɗi ko sakamakon samunsa ko kuma a halin rashinsa. Ana sa ran wannan nazarin zai taimaka wurin fito da wani tsarin bin diddigin nazarin halayyar ɗan Adam ta daban musamman ga ɗalibai da masu nazari.

**Muhimman Kalmomi: -** Nazari, Hali, Ɗan Adam, Waƙa, Rayuwa
**Received**: 20/08/2025 Accepted: 23/09/2025 **GSM**: +234(0)8065380952 **Email:** sanusigambobeloo@gmail.com
**Corresponding Author:** Abdullahi, R. M.
**Article Citation**: Abdullahi, R. M. da Bello, S. G. da Yusuf, L. (2025).Nazarin Halaye da Ɗabi’un Mutane a cikin Waƙar *Kalar Rayuwa* ta Sadiq Abubakar Bello. *Jalingo Journal of Languages and Literary Studies (JAJ0LLS). 9 (4) pp. 153-164.*
**Publishers**: Department of Languages and Linguistics, Taraba State University, Jalingo. **ISSN**: 2488-9067

## 1.0 Gabatarwa

Masu iya magana kan ce “Hali zanen dutse” wannan batun haka yake, duba da cewa dukkan halittun da Allah (S.W.T) ya halitta kowa da irin nasa halin. Hali wata al’ada ce ta rayuwa da aka riga aka saba da ita. Al’ada kuwa ba komai ba ce face abin da rai ya riga ya saba da shi ya zama jikinsa, (Bunza, 2006: xxvii). Wannan shi ya sa kowane ɗan Adam yana da halinsa dangane da muhallin da ya tsinci kansa a ciki da irin tarbiyyar da ya samu a rayuwa. Irin tarbiyyar da mutum ya samu shi yake masa jagoranci a halayyarsa da kuma tunaninsa waɗanda yake bayyana su a cikin ayyukansa da maganganunsa na yau da kullum da kuma irin fiƙirorin da Allah ya albarkace shi da su na daga ayyukan adabi kamar waƙoƙi da zube da sauransu. Ayyukan adabin Hausa cike suke da bayyana halayen al’umma iri-iri, sawa’un waɗannan halayen kyawawa ne ko kuwa akasinsu.

A wannan takarda, an yi ƙoƙarin bin diddigin halayyar ɗan Adam sau-da-ƙafa a cikin rubutacciyar waƙa mai taken "Kalar Rayuwa" domin nazartar ire-iren halayen da suke ƙunshe a cikinta.

## 1.1 Taƙaitaccen Tarihin Mawaƙi

An haifi mawaƙin wato Sadiq Abubakar Bello a ranar Laraba 22 ga watan Agusta, 1990 a garin Mutum-biyu cikin ƙaramar hukumar Gassol Jihar Taraba. Ya fara karatun Alƙur'ani mai girma a makarantar malam Babaji a hanun malam Abbas, inda daga ƙarshe ya yi saukan Al'ƙur'ani a wurin maƙwabcinsu malam Sani Barjanga lokacin yana da shekara goma sha biyu (12). Sannan ya yi karatun litattafai a wurin maluma da dama, cikinsu akwai malam Abubakar Dadangodo da malam Sabo Zango da malam Yahuza Abubakar da sauransu. Ya yi karatun firamarensa a Central Primary School Mutum-biyu, sannan ya yi Sakandarensa a Lugga Government Day Secondary School, Mutum-biyu inda ya kammala a shekarar 2007. Bayan gama Sakandarensa ya sami gurbin karatu a Kwalejin Horar da Malamai (College of Education) da ke Jalingo (kafin daga bisani a mayar da shi Zing), ya kammala a shekarar 2011. Ya tafi Jami'ar Bayero da ke Kano inda ya sami digirinsa na farko sashen koyar da harsunan Nijeriya (Hausa) a 2017. Yanzu haka shi malami ne a Kwalejin horar da malamai (College of Education) da ke Zing kuma yana da aure.

Mawaƙin ya fara waƙa a shekarar 2007 a auren wani abokinsa. Sai dai bayan ci gaba da waƙarsa, sai ya fi karkata kan waƙoƙin siyasa. Amma hakan bai hana shi yin waƙoƙin aure da na suna da na sarauta da na faɗakarwa da na soyayya da sauransu ba. A taƙaice dai, shi mawaƙin gama-gari ne.

## 1.2 Maƙasudin Waƙa

Mawaƙin ya lura da inda da yawa daga cikin masu kuɗinmu na wannan zamani, za ka samu kuɗaɗansu ba ta hanyar Allah da Annabi ba ne suka tara su ba. Musamman ma matasanmu, inda idan ma'aikacin gwamnati ne za a samu sata ya yi ya tara su masu yawa. Idan kuma ɗan siyasa ne, shi ma kazalika. Har ma da 'yan kasuwanmu, su ma ba a bar su a baya ba wurin saɓa wa Allah domin su tara dukiya, da ma sauran al'umma. Duba da irin wannan da kuma halin da al'umma ta tsinci kanta a wannan zamanin saboda kuɗi. Wannan shi ne babban maƙasudin yin wannan waƙa.

## 1.3 Ra'in Bincike

Wannan aikin an ɗora shi ne a kan *Ra'in Zahiranci.* Wannan ra'i an ƙirƙiro shi ne a shekarar 1830 a Faransa. Waɗanda suka kirƙiro kuwa su ne Gustave Flubert da Honor da Belzac da George Eliot da Adam Bede (1859) da sauransu. Ra'in na ɗaya daga cikin mazahabobin tarken adabi da ke duba wasu abubuwa na rayuwa a cikin al'umma, musamman rayuwa ta zahiri, kuma ta samu karɓuwa ga matarka masu sha'awar duba halayen al'umma daban-daban. Bayan bullowar wasu matarka masu la'akari da halayen zahiri a cikin litattafan hira da na wasan kwaikwayo/fim da kuma waƙa. Suna fito da wasu halayyar rayuwa na mutane a cikin al'umma na zahiri. Marubuta da dama suna yin rabuce-rubuce game da halin rayuwar al'ummar Hausawa dake gudanarwa a zamaninsu, don ƙoƙarin fito da wasu matsalolin da ke aukuwa a cikin al'ummar da nufin a magance su. Wasu matsalolin kirkirarsu aka yi, kuma suna da nasaba da halin rayuwar da mutum ya sami kansa ya kuma kasa daurewa (Levin, 1965:276). Daga cikin manufofin mazahabar akwai: Kimanta duniyar ɗan'adam da abin da ke faruwa a cikinta, da son bayyana su yadda ya dace da nazarin halayen ɗan adam da wasu abubuwan da tunani ke tsinkaya na rayuwar yau da kullum, kamar siffanta halin rayuwa na gaskiya (na zahiri) da yadda ake ba ta muhimmanci da kuma nuna faruwar abubuwan zahiri a cikin al'umma kamar wahala da musgunawa da danniyar shugabanni da haɗama don neman tara abin duniya.

Saboda haka, akwai wasu matsaloli da dama da ake fuskanta, waɗanda a zahiri suke wakana a cikin al'ummar Hausawa. Mutane ne ke aiwatar da su a fili ga su nan ana gani ƙuru-ƙuru.

Yawanci mutane ne masu ƙarancin haƙuri da rashin tunanin gaba, musamman na abin da za a samu ko wanda ake hange a rayuwa.

**1.4 Hanyoyin Tattara Bayanan Bincike da Yin Nazarinsu**

An tattaro bayanan wannan bincike ne ta hanyar sauraron waƙar da farko, sannan aka rubuta ta a takarda domin samun damar tsettsefe ire-iren halayen da ke ƙunshe ciki domin yin nazarinsu. Dangane da hanyoyin da aka bi don yin wannan nazari kuwa, an yi amfani ne da hanyoyi guda biyu. Wato hanya ta farko ita ce ta binciken ayyukan da magabata suka gabatar masu alaƙa da wannan nazari, kamar bugaggun litattafa da kundayen bincike da jaridu da maƙalu da sauran litattafan ilimi. Hanya ta biyu kuma ita ce inda aka yi amfani da sharhantau (Descriptive Analysis) wajen ƙalailaice bayani game da abin da aka zaƙulo na daga halayyar ɗan Adam a cikin waƙar da ake nazarinta.

**2.0 Ma'anar Waƙa**

Masana da manazarta da dama sun bayyana ma'anar rubutacciyar waƙa a cikin aikace=aikacensu na adabi kamar Muktar (2005:2) ya bayyana rubutacciyar waƙa da cewa "Wata hanya ce ta gabatar da wani saƙo a cikin ƙayyadaddun kalmomi da aka zaɓa waɗanda ake rerawa a kan kari da ƙafiya a cikin baitoci". Shi kuwa Ɗangambo (2007:5) ya bayyana ta da cewa "Waƙa wani saƙo ne da aka gina shi kan tsararriyar ƙa'ida ta baiti, ɗango, rerawa, kari (bahari), amsa-amo (ƙafiya) da sauran ƙa'idojin da suka shafi daidaita kalmomi, zaɓensu da amfani da su cikin sigogin da ba lalle ne haka suke amaganar baka ba". Shi kuma Sa'id (2002) ya bayyana rubutacciyar waƙa da cewa "Tsara ta ake yi bisa wasu tsayayyun ƙa'idoji, a kuma rubuta ta". Ke nan za a iya cewa waƙa ta bambanta da zance na yau da kullum ta fuskar tsarawa da bin wasu ƙa'idoji.

**2.1 Ma'anar Hali**

Masana da dama sun bayyana ma'nar hali ta fuskoki daban-daban kamar Dumfawa (2011) inda ya kalli ma'anar hali da ɗabi'a sannan ya ce "Ɗabi'a na nufin wata halayya da ta ƙunshi son kai". Sannan ya ƙara da cewa wannan wata ɗabi'a ce ta ɗan Adam face idan ya sha wani magani mai raba shi da ita. Hankali da tunanin abu kan kasance daidai da yadda ɗabi'ar abin take, wannan shi ke sa abubuwa irin rowa da kwaɗayi kan bayyana a fili. Shi kuwa Bunza (2006:xxvi) ya kalli hali a matsayin "Wani abu ne da Bahaushe ke dangantawa da sababben abu. Hali yana da makusanciyar ma'ana da "al'ada" domin a ganin wasu al'adar abu shi ne halinsa". Sannan ya ƙara da cewa Bahaushe ya lura da cewa, hali a cikin jini yake don haka yake hangen hali a wasu fukoki da yawa cikin zantukansa na yau da gobe irinsu: "Hali zanen dutse" da "Mai hali ba ya barin halinsa" da "Rai da hali ba a raba su" da "Halin uwa ɗiya kan ɗauka" da "Hali abokin tafiya". A CNHN (2006:191) an bayyana hali a matsayin lokaci ko yanayi ko kuma ɗabi'a musamman ta mutum".

Dangane da bayanan da suka gabata, za mu iya bayyana hali da cewa wani tambari ne da ake iya gane halitta da shi ta fuskar yanayin da yake tsintar kansa ko ɗabi'unsa da ba wanda ya isa ya iya raba shi da su sai mahaliccinsa. Akasarin masana da manazarta a nazarce-nazarcensu sun fi kallon hali ta fuskar ɗabi'a a yayin bayar da bayanansu ko kuma wurin gudanar da nazarce-nazarcensu. Ƙudirin wannan takarda ne yin nazarin halayyar ɗan Adam a cikin waƙar Kalar Rayuwa ta fuskar ɗabi'a da kuma yanayi kamar yadda suka bayyana cikin waƙar.

**3.0 Nazarin Halayyar Ɗan Adam Cikin Waƙar *Kalar Rayuwa***

Nazarce-nazarce da dama sun gudana daga masana da manazarta, inda suke ƙoƙarin zaƙulo halayyar ɗan Adam a cikin rubuce-rubucensu na ilimi da kuma ayyukan da suka shafi adabin Hausa irin su zube da waƙoƙi da kuma wasannin kwaikwayo. Masana irin su Kirk-Greene (1973) da Alhassan da Musa da Zarruƙ (1983) da Yahaya da Zariya da Gusau da 'Yat'aduwa (1992) da Adamu (2001) da Muktar (2006) da Bara'atu Inuwa Maikadara (2012) da Nafisa Usman Tafida (2017) duk sun yi nazarin halayyar ɗan Adam da suka ƙunshi kyawawan

halaye da kuma munana. Kyawawan halaye sun haɗa da tausayi da kunya da gaskiya da ladabi da biyayya da haƙuri da amana da sauransu. Yayin da munana kuma sun ƙunshi irin su kwaɗayi da butulci da cin amana da gulma da mugunta da hasada da sauransu. Ta la'akari da nazarce-nazarcen da masana suka gabatar, wannan takarda zai yi ƙoƙarin fito da halayen da ke cikin waƙar Kalar Rayuwa domin yin nazarinsu, sannan a fito da baitukan da suke ɗauke da waɗannan nau'in halayen da ake magana a kansu kamar haka:

### 3.1 Gaggawa

CNHN (2006:150) ya bayyana gaggawa da" Hanzari". Hanzari kuwa na nufin "motsawa da sauri wajen yin wani abu". Gaggawa kalma ce da ake iya amfani da ita ta fuskoki biyu da ya ƙunshi lamari mai kyau da kuma mummuna. A lamari mai kyau, idan an aiki yaro kuma ana bukata da wuri sai a ce masa ka yi gaggawa wato ya je ya dawo da wuri ke nan ko kuma wurin aikin alheri a sha'ani na addini da sauransu. A ɓangaren mummuna kuwa, daga ciki akwai abinda ya shafi rabo na rayuwa wanda yake tafiya da lokaci, kuma ko badaɗe ko bajima zai iso ga mutum, idan mutum ya zaƙe ko ta halin ƙaƙa ya ga ya samu sai a ce masa ya fiya gaggawa. Wanda hakan kuwa ya saɓa da addini da addini da kuma al'adar Bahaushe, shi ya sa suke cewa "Gaggawa aikin sheɗan". Ga abin da wannan baitin nan yake cewa:

***Mai son arziƙinsa nan take sai ya je ya yi kuɗin jini***
*Mutani su fara ƙosawa su ɗau alhakin wani*
*Da ya ba su sais u hau karɓa su ce sun ji sun gani*
*Gari su yi fadi a kayinsa dalilin taro-taro.*

A ɗango na farko cikin baitin, mawaƙin ya nuna yadda idan mutum yana son ya yi arziki da wuri, wato "Nan take" sai ya je ya yi kuɗi ta hanyar saɓon Allah (S.W.T). "Ya je ya yi kuɗin jini", wato kuɗi ta hanyar tsafi ko bin bokaye da makamantansu, maimakon ya jira wa'adinsa da Allah ya ɗeba masa na yin arziƙi. Yin hakan ɗabi'a ce ta gaggawa.

### 3.2 Zargi

Zargi lamari ne da yake ɗarsuwa tun daga zuciya har zuwa furucin ɗan Adam. Bargery (1934:1134) ya bayyana zargi da cewa "Yin furuci ko magana kan wani lamarin da ya faru a halin rashin tabbaci". Irin wannan ɗabi'a ya kasance jini da tsoka wurin wasu mutane da ba za a iya raba su da ita ba. Kuma addini ya yi hani da yin sa, domin gudun ɗaukan alhakin wanda bai ci ba bai sha ba, har ma yake cewa "zato zunubi ne ko da ya kasance a kan gaskiya ne". Za mu ga inda mawaƙin ya bayyana shi cikin baitin da ke ƙasa kamar haka.

*Mai son arziƙinsa nan take sai ya je ya yi kuɗin jini*
***Mutani su fara ƙosawa su ɗau alhakin wani***
*Da ya ba su sai su hau karɓa su ce sun ji sun gani*
*Gari su yi fadi a kayinsa dalilin taro-taro.*

Ɗango na biyu na baitin, ya fito da zargi a fili inda ya nuna yadda mutane za su "ƙosa" wato shiga halin damuwa na ganin sun san ta yaya ya sami kuɗin wanda zai kai su da har su ɗauki alhakin wani ta hanyar rashin tabbas. Wannan ne ya sa addani ya yi hani da yin sa domin irin wannan kan iya haddasa fitina.

### 3.3 Kwaɗayi

Kwaɗayi wani abu ne da yake shiga zuciya musamman dangane da nama, kuɗi da kuma mata (Bargery, 1934:666). Ita kuwa Umma Ado Inuwa (2000:70) ta bayyana kwaɗayi ne da zarmewar zuciya. Kwaɗayi mummunan hali ne a tsarin tarbiyyar Bahaushe, don haka ne ma Hausawa ke ƙoƙari wurin nusar da 'ya'yansu aibun da ke tattare da wannan ɗabi'a domin su guje mata. Wannan ta sa Bahaushe yake azancin magana da ke cewa "Kwaɗayi mabuɗin wahala", kamar yadda za mu gani a baitukan da ke suke zuwa kamar haka:

*Mai son arziƙinsa nan take sai ya je ya yi kuɗin jini*
*Mutani su fara ƙosawa su ɗau alhakin wani*
***Da ya ba su sai su hau karɓa su ce sun ji sun gani***
***Gari su yi fadi a kayinsa dalilin taro-taro***

A wannan baiti ɗango na uku zuwa na huɗu, mawaƙin ya fito da yadda mutane suke nuna kwaɗayin kuɗinsu a fili inda daga ya ba su sai su hau karɓa ba ji ba gani duk da yake ba su san yadda ya samo su ba, wanda hakan ma kan iya kai su da yin faɗa da junansu ko da wasu saboda kuɗin da yake ba su ko idan waɗansu za su aibanta shi.

*Kalar rayuwa, kalar rayuwarmu kwai tsada*
***Maganar mai kuɗi ake yarda***
*Halin ɗan Adam ka ƙyale shi*
*Kuɗi yanzu sai ya canza shi, musamman taro-taro.*

Wannan baiti kuma, ɗango na biyu ya nuna a rayuwan nan mutum idan yana da kuɗi to shi ke nan duk abin day a faɗa ya ci ya sha ko da kuwa ƙarya ce saboda yana da kuɗi kuma yana ba su.

### 3.4 Son Zuciya/Kai

Son kai shi ne mutum ya fi son kansa fiye da komai, ta inda ba zai iya haƙuri da wani abu ba. In dai ba kansa ba ne to kowa ya haƙura (Nafisa Usman Tafida, 2017:93). Kenan, son kai rauni ne na zuciya da kan sanya mutum aikata komai domin biyan bukatan kansa ba tare da la'akari da bukatun wasu ko halin da za su shiga ba. Za mu ga hakan a wannan baitin inda yake cewa:

***Ga boko haram a nan ma a kwantiraki sun ɗan riƙo***
*Suka fitad da Shehu mulkanmu haɗa masu yin dako*
***Da ma masu yin fashin daji gari fa sun tsallako***
*Su ma don kuɗi suke aikinsu sisi taro-taro.*

Baitin naƙoƙarin bayyana mana irin gubar da ke tattare da son zuciya, inda ya nuna cewa wasu sun karɓo kwantiraki, wato kwangilar kafa ƙungiyar mayaƙan Boko Haram waɗanda su aikinsu shi ne yaƙar waɗanda ba su ci ba ba su sha ba kawai domin cimma wasu bukatunsu. Sannan a ɗango na uku ya nuna irin yadda ɗabi'ar fashi da makami ya ƙaru, inda da a daji suke yi yanzu abin ya fantsama har sun shigo gari, wannan ya sa duk ba wanda ya tsira don kawai biyan bukatun kansu.

### 3.5 Butulci

Butulci kalma ce da ta samo asali daga sunan mai yin ta wato "Butulu". Bargery (1934:141) ya bayyana ta da "Rashin godiya". Bunza (2015) ya bayyana wasu fuskokin da za a fahimci butulu da su, daga cikinsu ya kasance: ya ɓata wanda ya taimake shi, ko ya cutar da shi ta hanyar amfanin da ya samu gare shi. A tsiri aƙidar sa ƙafan wando ɗaya da shi a kowace rawa zai taka. Ke nan, butulu kaza ne mai ci ya goge baki kamar yadda za mu gani a baiti na 8 kamar haka:

*Biyayya a ma ta 'yan gangan kamar masu gaskiya*
*Ka ɗauka wa kai ake ƙauna ka harɗe wuri ɗaya*

***In ka ba su sai su gode in ka ƙi su yi ashariya***
***kuɗin wassu kan na rowa ne ka furta su hanƙaro.***

A wannan baiti kuma,ɗango uku zuwa na huɗu suna ƙoƙarin fito mana da mummunar ɗabi'ar ɗan Adam na butulci inda idan kana yi masa kyauta to ba wani kamar ka. A duk lokacin da ya zo ka nuna babu to ka zamo abokin gaba.

### 3.6 Tozarci

Allah (SWT) ya bayyana cewa ya karrama bil-Adam sannan ya yi umurni da kyautatawa a dukkanin mu'amala da kuma zamantakewa tsakanin 'yan uwa ko mata da miji da sauransu. Amma wasu saboda da wata dama ta abin duniya burinsu a kullum su ga wasu sun tozarta. CNHN (2006:440) yabayyana tozarta da "Wulaƙanci". Wulaƙanci kuwa na nufin rashin daraja mutum ko abu, kamar yadda za mu gani cikin baitin da ke biye.

*A kan 'yar kuɗi ƙalilan sai ku ɓata da 'yan uwa*

*Mutum sai ya rinƙa girman kai kamar mai zubo ruwa*
***Sannan bai da lokacin matarsa ya sa ta makkuwa***
***Kullum zuciya tana saƙe-saƙe ta sami kwarkwaro.***

A wannan baiti, ɗango na uku da na huɗu suna ƙoƙarin fito mana da irin ɗabi'ar da wasu masu mutane suke nuna wa iyalansu na rashin kula da muzantawa a dalilin sun sami kuɗi wanda zai iya kasancewa bah aka bane a lokacin da bai da su. Irin wannan kan sanya iyalan shiga damuwa musamman ma matansu duba da yadda mata suke da rauni.

### 3.7 Yaudara

Yaudara tana daga cikin munanan halaye da ɗabi'un ɗan Adam wadda takan iya kai shi ga halaka. Yaudara na nufin hali na ɓoye gaskiya da niyyar cuta ko zambatar wani (CNHN, 2006:480). Kenan, duk wanda ya kasance mai ɓoye haƙiƙanin abin da ke ransa ya bayyana akasin haka domin biyan wani bukatarsa za a kira shi da mayaudari kenan; kamar yadda ya zo cikin baitukan da ke biye.

***Biyayya a ma ta 'yan gangan kamar masu gaskiya***
***Ka ɗauka wa kai ake ƙauna ka harɗe wuri ɗaya***
*In ka ba su sai su gode in ka ƙi su yi ashariya*
*kuɗin wassu kan na rowa ne ka furta su hanƙaro.*

Wannan baiti, ɗango biyun farko na ƙoƙarinbayyana wani hali daga munanan halayen ɗan Adam na yaudara. Mawaƙin ya bayyana yadda mutane suke wa masu kuɗi ladabi da biyayya na ƙarya kamar suna ƙaunarka, su kuwa abin hannunka kawai suke bukata da zarar babu su sais u gudu su bar ka. Shi ne abin nan da Hausawa ke cewa ladabin kule idan ya hangi ɓera.

*Siyasa kuɗi ake wabta*
*Ko da ko ana ta tatata*
*Akwai masu nuna jarunta*
*Su sato su zo su alkinta*
***Mu ko sai su ringa burge mu***
***Ana banzatar da haƙƙinmu***
*A kan kuma kuɗi suke wannan, da hujja na tattaro.*

Wannan baitin ya fito mana da irinɗabi'un 'yan siyasarmu, ta yadda kuɗaɗen da suka tattara ma haƙƙoƙin talakawa ne da aka ba su domin a yi musu ayyuka amma suka handame suna gina manyan gidaje da hawa manyan motoci da sauransu suna yawo a gari har suna burge wasu bayan kuma ƙarya ce da yaudara.

*Mulkin mallaka da ka lura*
***Da an kai ƙwarai akwai ƙura***
***Kuɗaɗenmu sun ka tattara***
*Yaƙin duniya ku dudduba*
*Abin ai ba za ya ƙare ba*
*A kan dukiya suke gaba*
*Da za ai shiru a saurara*
*Akwai mai awarwaro.*

Turawa sun shigoƙasashenmu sannan sun mulke mu, sai dai da akwai yaudara a tsarin mulkin nasu inda mawaƙin ya kira ta da **Ƙura** duba da cewa sun hangi ɗimbin dukiya da albarkatun da muke da su ne suka zo suka kwashe suka kai ƙasashensu. Irin wannan yaudarar ta Turawan mulkin mallaka har yanzu bamu kuɓata daga gare ta ba saboda har yanzu suna ta haɗa mu faɗa sannan suna sa shuwagabanninmu suna kwashe dukiyar ƙasarmu suna kai musu.

### 3.8 Haɗama

Haɗama na nufin ɗabi'ar son kwasuwar abu da yawa fiye da sauran jama'a a wajen rabo (CNHN, 2006:188). Wannan ɗabi'a na son kwasar abu fiye da kowa ya zamo zamo ruwan dare a wannan zamani domin ba wanda ya bari. Bai bar masu kuɗi ba, bai bar talaka ba, bai

bar shuwagabanni ba inda kowa burinsa ya ɗiba ya tara ko da ko bazai yi amfani da shi ba kamar yadda za mu gani cikin baitukan da ke biye.

***Siyasa kuɗi ake wabta***
*Ko da ko ana ta tatata*
*Akwai masu nuna jarunta*
***Su sato su zo su alkinta***
*Mu ko sai su ringa burge mu*
*Ana banzatar da haƙƙinmu*
*A kan kuma kuɗi suke wannan da hujja na tattaro.*

Wannan baiti kuwa, na ƙoƙarin nuna mana irin halin haɗama na ɗan Adam musamman wurin 'yan siyasarmu inda ya kasance fage ne da suke kwashe kuɗaɗe ko ta halin ƙaƙa su tattara su ko da ko ba za su ci ba, a halin ga masu bukata.

*Su 'yan kasuwanmu ma duba haɗa masu kwangila*
*Da ma malamai na addini da bokon gala-gala*
*Ma'aikatanmu yanzu aikinsu su sassace ƙwandala*
***Kowa so yake ya tattara ya zauna ya yo shiru.***

Wannan baiti na ƙoƙarin nuna mana yadda wannan hali na haɗama ya zamo ruwan dare tsakanin al'umma, ba ga 'yan kasuwa ba zuwa ga 'yan kwangila da malaman addini da na boko har ma da ma'aikta, kowa burinsa ya sami dammar samun kansa a muhallin dukiyar jama'a domin ya kwashi nasa rabon.

### 3.9 Rashin Tabbas

Wani mawaƙi yana cewa "Ɗan Adam mai wuyan gane hali". Haka nan, masu hikimar magana kan ce "Ba a gama halittan mutum ba sai ya yi kuɗi" domin a wannan lokaci ne asalin siffarsa da halayyarsa za su bayyana. Rashin tabbas wani yanayi ne da ya ƙunshi rashin iya bayyana haƙiƙanin halin mutum a yayin da yake cikin wani hali na rayuwa domin yana iya canzawa saboda wani dalili, kamar yadda za mu gani cikin baitukan da ke biye.

***A kan 'yar kuɗi ƙalilan sai ku ɓata da 'yan uwa***
***Mutum sai ya rinƙa girman kai kamar mai zubo ruwa***
*Sannan bai da lokacin matarsa ya sat a makkuwa*
*Kullum zuciya tana saƙe-saƙe ta sami kwarkwaro.*

A ɗango na farko da na biyu na wannan baiti, suna nuna mana yadda kuɗi ke canza halin ɗan Adam ya sa shi ya ɓata da 'yan uwansa ko da ko sun taimaka masa a baya. Kenan, ya zamo abin nan da Hausawa ke cewa "ɗan tsako samu ƙwaya ka ƙi dangi". Haka nan, yakan mayar da shi ya zamo mai girman kai wanda Hausawa kan ce "Rawanin tsiya".

*Kalar rayuwa, kalar rayuwarmu kwai tsada*
*Maganar mai kuɗi ake yarda*
***Halin ɗan Adam ka ƙyale shi***
***Kuɗi yanzu sai ya canza shi, musamman taro-taro.***

A wannan baiti, ɗango na uku da na huɗu suna bayyana mana yadda kuɗi yake da matuƙar tasiri a kan ɗan Adam wurin saurin canza masa hali. Irin wannan za mu iya gani a rayuwar zamantawarmu na yau da kullum.

### 3.10 Ɓarna

Ɓarna kalma ce da take da ma'ana ta al'ada da kuma ta addini. A al'adance Kalmar tana nufin ta'adi; ita kuwa ta'adi na nufin ɓarna ta ganganci ko cuta ko lalata CNHN (2006:461). A addinance kuwa tana nufin taka dokar Allah (S.W.T) ta hanyar aikata manyan laifuffuka kamar zina da shan giya da kisa da sauran manyan laifuffuka. Haka kuma dawwama a kan ƙaramin laifi kamar kallon mata ko taɓa su (Kabara, 2009:71). Za mu iya ganin wannan a baitin da ke biye kamar haka:

*An ce zamani yana zawwa*
*Aike za a aikewa*

***Haram ko halak a badawa***
*A neman abinci bayarwa*
***Mutane su rinƙa yin zamba***
***Kisa ba abin nadama ba***
*Hakan babu yaro ko bubba*
*A neman kuɗi ake wannan jawabin na cicciro.*

A wannan baitin, mawaƙin ya yi ƙoƙarin bayyana wani halin ɗan Adam na son aikata laifi sai dai wanda Allah ya tsare. Allahu Subhanahu Wata'ala ya bayyana cikin Alƙur'ani mai girma cewa a ƙarshen zamani ɓarna za ta yawaita a bayan ƙasa. Mawaƙin ya yi ƙoƙarin fito da wasu laifukan da ake aikatawa waɗanda al'umma ke ɗaukan su ba komai ba kamar rashin tantance halak wurin nema da zamba da kuma kisa ba tare da dalili ba, wanda a yau ya zamo ruwan dare.

**3.11 Rashi**

Wannan wani hali ne da mutum ko mutane kan shiga a sakamakon wani yanayi na rayuwa. Akasari, irin wannan yanayin kan jefa wasu cikin halaka. Bargery (1934:844) ya bayyana rashi da *"Lack"*. Cambridge International Dictionary of English (1995:696) ya bayyana *Lack* da:

*"To not have or not have enough of something that is needed or wanted"*

*Fassara:*

*Rashi shi ne ya kasance babu abu gaba ɗaya ko akwai ƙarancin abin da ake bukata ko nema*

Kenan, rashi ba lallai sai babu abu gaba ɗaya ba, har ma da idan ya kasanceakwai abin amma bai wadata ba duk suna iya kasancewa rashi. Ga yadda al'amarin yake:

***Hatta masu karuwanci ma kuɗi ne fa sun ka so***
***Domin babu ci da shan rana dare a gidan wasu***
*Da sun yo kuɗi su koma wa iyayensu ƙara so*
*Ɗawainiyar gidan su ɗauke wa iyayensu na shiru.*

Karuwanci mummunar ɗabi'a ce wadda Allah ya yi hani da aikata ta sannan al'adar Bahaushe ta ƙyamace ta. A rayuwa ba wanda zai so ya ga ahalinsa cikin wannan hali, amma rashi kan jefa wasu 'ya'ya cikin wannan hali inda suke zuwa don su samo kuɗaɗe su kai wa iyayensu, maimakon su yi musu faɗa sai su kasance abin soyuwa a gare su kamar yadda baitin ya nuna.

**3.12 Jarabta**

Duk yanayin da ɗan Adam ya tsinci kansa a cikinsa, haƙiƙa da akwai dalilin da Allah Subhanahu Wata'ala ya bar shi a hakan sannan yakan iya jarabtarsa ta kowane hali a duk lokacin da ya ga dama. Jarabawa a nan na nufin gwada ƙarfin imanin da Allah (SWT) yake yi wa bayinsa. Ita ma wannan wata nau'i ne na hali da yanayi ke haifar da shi. Ga yadda abin yake a baitin da ke biye.

***Haƙiƙa kuɗi masifa ne***
***Babu su kata'i ne***
*Ko'ina kuke zaune*
***Rayuwa ta yo tsami***
***Kaya sai su kama yin tsada***
***Gashi yanzu ba yarda***
*Duk ka zam kamar danda*
*Har gida a ma hauro.*

Allah Subhanahu Wata'ala ya bayyana a cikin Alƙurani mai girma cewa shi fa kuɗi fitina ce sannan ya umurce mu da mu nemi tsari da talauci. Kenan, duk halin da mutum ya tsinci kansa a ciki wata jarabawa ce, mafitar ita ce ya koma ga Allah. Haka nan, za mu ga yadda mawaƙin ya bayyana kuɗi cikin baitinsa da masifa sannan ya kira rashinsu (wato talauci) da kata'i, inda a duk inda kake walau mai kuɗi ko talaka rayuwar babu daɗi. Sannan ya sake bayyana mana

wata jarabawar ta tsadar kaya da kuma halin tsoro na rashin yarda saboda kowa bai yarda da ɗan uwansa ba. Duk waɗannan na daga cikin jarabce-jarabcen da Allah yake jarabtan bayinsa.

**4.0 Kammalawa**

A wannan nazari, an yi ƙoƙari wajen fito da wasu halayyar ɗan Adam cikin waƙar Kalar Rayuwa ta Sadiq Abubakar Bello. Takardar kamar yadda ta nuna, mawaƙin ya yi amfani da fasaharsa wajen bayyana halayya mabambantan cikin waƙarsa ta fuskar ɗabi'a da kuma yanayi. A ɓangaren ɗabi'a, an gano halaye irin su gaggawa da zargi da kwaɗayi da son zuciya da butulci da tozarci da yaudara da haɗama da ɓarna da kuma rashin tabbas. Sa'annan ta fuskar yanayi kuwa, nazarin ya gano yanayi na rashi da kuma jarabta, duk waɗannan sun bayyana cikin wannan waƙa ta Kalar Rayuwa.

## Manazarta

Adamu, A.U (2001). Tarbiyar Bahaushe Mutumin Kirki and Hausa Prose Fiction: Towards an Analytical Framework.

Alhassan, H. da Musa, U.I da Zarruƙ, R.A. (1982). *Zaman Hausawa (Bugu na Biyu don Makarantun Gaba da Firamare).* Islamic Publications Bureau.

Bergery, G.P (1993). A Hausa-English Dictionary and English-Hausa *Vo*cabulary. Oxford University Press.

Bunza, A.M (2006). *Gadon Feɗe Al'ada*. Tiwal Nigeria Limited, Surulere.

Bunza, A.M (2005). "In an ci Moriyar Ganga a Ba ta Tukuicin Girma (Awon Nauyin Butulci a Duniyar Tunanin Bahaushe Tsakanin Adabi da Haƙiƙa)". Takardar da aka gabatar a babban taron ilimi na bukukuwan Sati Ɗaya ƙarƙashin *Score Card Committee* na Jami'ar Umaru Musa 'Yar'adu'a domin jinjinawa da ɗebe kewar Farfesa Mu'uta Ibrahim; mataimakin shugaban Jami'ar mai baring ado a babban Ɗakin Taro na Jami'ar.

CNHN. (2006). *Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero*. Zaria: ABU Press.

Cambridge International Dictionary of English (1995). *New Cambridge Advanced Leaner's Dictionary*. Cambridge University Press.

Ɗangambo, A. (2007). *Ɗaurayar Gadon Feɗe Waƙa*. Kano: K.D.G Publishers.

Kabara, Y.S (2009). Fassara da Bayanan Wasu Kalmomin Laifuffuka da Mu'amala na Musulunci zuwa Hausa. Kundin Digiri na Biyu, Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya; Jami'ar Bayero, Kano.

Kirk-Greene, A.H.M (1973). Mutumin Kirki:The Concept of the Good Man in Hausa. A paper Presented in the Third Annual Hans Wolff Memorial Lecture Delivered at the University of Indiana.

Maikadara, B.I (2012). Tarbiyya a Rubutattun Waƙoƙin Hausa na Ƙarni na Ashirin. Kundin Digiri na Biyu, Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya; Jami'ar Bayero, Kano.

Muktar, I. (2005). *Bayanin Rubutattun Waƙoƙin Hausa*. Abuja: Countryside Publishers Company.

Sa'id, B. (2002). Tasirin Larabci A Kan Rubutattun Waƙoƙin Hausa. Algaita Journal of Current Reaseach in Hausa Studies. Vol. 1 No. 4 pp. 130 – 145

Tafida, N.U (2017). Wasu Halaye da Ɗabi'un Matan Ƙasar Zazzau. Kundin Digiri na Biyu, Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya; Jami'ar Bayero, Kano.

Yahaya, I.Y da Zariya, M.S da Gusau, S.M da 'Yar'aduwa, T.M (1992). Darussan Hausa Don Manyan Makarantun Sakandare, Littafi Na Uku. Ibadan: University Press PLC.

## Rataye

**WAƘAR KALAR RAYUWA TA SADIQ ABUBAKAR BELLO**

**Amshi:** Haƙiƙa kuɗi masifa ne a wannan gidan aro
Muna ƙoƙari mu tara su ko da sisi taro-taro.

1. Allah wahidun ilahina da kai ne na sallamo
Ka min taimako a aikina jawabi na kinkimo
Salati wurin rasulullahi mai kyau da kyan amo
Sako alihi sahabati bayani na tattaro.
2. Mai son arziƙinsa nan take sai ya je ya yi kuɗin jini
Mutani su fara ƙosawa su ɗau alhakin wani
Da ya ba su sais u hau karɓa su ce sun ji sun gani
Gari su yi faɗi a kayinsa dalilin taro-taro
3. Haƙiƙa kuɗi masifa ne
Babu su kata'i ne
Ko'ina kuke zaune
Rayuwa ta yo tsami
Kaya sai su kama yin tsada
Gashi yanzu ba yarda
Duk ka zam kamar danda
Har gida a ma hauro.
4. Ga boko haram a nan ma a kwantiraki sun ɗan riƙo
Suka fitad da Shehu mulkanmu haɗa masu yin dako
Da ma masu yin fashin daji gari fa sun tsallako
Su ma don kuɗi suke aikinsu sisi taro-taro
5. Hatta masu karuwanci ma kuɗi ne fa sun ka so
Domin babu ci da shan rana dare a gidan wasu
Da sun yo kuɗi su koma wa iyayensu ƙara so
Ɗawainiyar gidan su ɗauke wa iyayensu na shiru
6. An ce zamani yana zawwa
Aike za a aikewa
Haram ko halak a badawa
A neman abinci bayarwa
Mutane su rinƙa yin zamba
Kisa baa bin nadama ba
Hakan babu yaro ko bubba
A neman kuɗi ake wannan jawabin na cicciro.
7. A kan 'yar kuɗi ƙalilan sai ku ɓata da 'yan uwa
Mutum sai ya rinƙa girman kai kamar mai zubo ruwa
Sannan bai da lokacin matarsa ya sat a makkuwa
Kullum zuciya tana saƙe-saƙe ta sami kwarkwaro.
8. Biyayya a ma ta 'yan gangan kamar masu gaskiya
Ka ɗauka wa kai ake ƙauna ka harɗe wuri ɗaya
In ka ba su sai su gode in ka ƙi su yi ashariya
kuɗin wassu kan na rowa ne ka furta su hanƙaro.
9. Siyasa kuɗi ake wabta
Ko da ko ana ta tatata
Akwai masu nuna jarunta
Su sato su zo su alkinta
Mu ko sai su ringa burge mu
Ana banzatar da haƙƙinmu

A kan kuma kuɗi suke wannan da hujja na tattaro.

10. Su 'yan kasuwanmu ma duba haɗa masu kwangila
Da ma malamai na addini da bokon gala-gala
Ma'aikatanmu yanzu aikinsu su sassace ƙwandala
Kowa so yake ya tattara ya zauna ya yo shiru.

11. Mulkin mallaka da ka lura
Da an kai ƙwarai akwai ƙura
Kuɗaɗen mu sun ka tattara
Yaƙin duniya ku dudduba
Abin ai ba za ya ƙare ba
A kan dukiya suke gaba
Da za ai shiru a saurara
Akwai mai awarwaro.

12. Kalar rayuwa, kalar rayuwarmu kwai tsada
Maganar mai kuɗi ake yarda
Halin ɗan Adam ka ƙyale shi